# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na uku: Fara muhawara


Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Dauda: | ɗan shekara 17 |
| Layla: | 'yar shekara 16 |
| Saima: | 'yar shekara 16 |
| Fada Bana: | ɗan shekara 49, kawun Dauda |
| Maigida Ranau: | ɗan shekara 51, baban Dauda |

**MAI GABATARWA:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wani sabon shirin na "Ji Ka Karu", kashi na uku daga cikin kashi goma na wasan kwaikwayonmu mai suna "Haɗin kan mutanen Sodangi", wanda aka shirya a kan yadda addini da siyasa suka haddasa zaman doya da man ja tsakanin wasu al'ummomi guda biyu, da kuma gidaje biyu. A cikin shirin da ya gabata abokan hirar tamu, wato matasan nan Dauda da Layla, sun fahimci cewa jagoranci a makaranta dabam yake da jagoranci a gida. A cikin kashin na yau mai suna "Fara muhawara" za ku ji yadda Saima ta ƙarfafa wa Layla gwiwa, da ta jajirce ta binciko tushen matsalolin da su Dauda suke fuskanta a gida.

**MAI BA DA LABARI:**

Shugabar wannan Kwaleji ta Zumunta, wato Malama Titi, ita ce ta kafa wannan Kungiya ta Muhawara tsakanin ɗalibai. Wannan mata, da ma tana ta tunanin yadda Kwalejin Zumunta za ta ciwo kofin nan da kowa yake haƙo, na muhawara mai 'yanci, wanda ake sa gasar cinsa kowace shekara. A halin yanzu, babbar sakandare ta Sodangi ce take riƙe da kofin. Don haka, shugabar kwalejin, wato Malama Titi, ta umarci Dauda da Layla a matsayinsu na shugabannin ɗalibai da su fara shirye-shirye. Da farko dai sai sun nemi ajin da za a yi amfani da shi a matsayin ofishin Kungiyar Muhawara.

**Fitowa ta 1: A Kwalejin Zumunta**

Dauda, Layla

**DAUDA:** To, wannan shi ne aji na ukun? Yaya kika gani?

**LAYLA:** Uhm, ai ya yi. Ai duk ya fi sauran. Dubi windunansa, gwanin sha'awa!

**DAUDA:** Kai, ba shakka! Ai kin ga ma hasken da ke shigowa ta windunan ya ƙara haskaka tunaninmu! Kai Malama Titi tana so ta ga irin abubuwan da za mu yi muhawara a kansu a wannan zangon karatun.

**LAYLA:** E to, ai ba za mu ari bakin sauran ɗalibai mu ci musu albasa ba. Yauwa Dauda, ina ganin mu shirya tambayoyi mana!

**DAUDA:** A'a! Waɗanne irin tambayoyi kuma?

**LAYLA:** Kamar a ce: "Faɗi abubuwan da suka dame ka daki-daki".

**DAUDA:** Kai, lalle ƙwaƙwalwarki na ja Layla! Abin ya yi! Kar ki ga yadda zan so na ji me za a ce.

**MAI BA DA LABARI:**
Shi fa gogan naku, wato Dauda, yana jin daɗin aiki da Layla. Da ganin fuskarsa za ka gane hakan! Shi kuwa Tafida, kishi ya lulluɓe shi. Sai ya yi ta saƙawa ina ma a ce shi ne! Na tabbata babansa ya yi azarɓaɓi da ya yi ƙoƙari ya ga a naɗa shi shugaban ɗalibai. A halin yanzu ba wata magana, tun da an riga an zaɓi Dauda, ba wani abu da zai iya yi. To, in kuwa yana so ya kusanci Layla, ba abin da ya rage illa ya shiga wannan Kungiya ta Muhawara. Hakan kuwa aka yi!

**Fitowa ta 2: A filin wasa**
Saima, Layla

**SAIMA:** Layla, ina jin a jikina Hassan yana kallonmu. Kai, wannan yaron ya cika ƙwaƙƙwafi.

**LAYLA:** Har gida yake raka ni Saima, ba a son ransa nake zuwa nan ba. Shi a tunaninsa bai kamata a ce ’ya mace tana wasannin motsa jiki ba.

**SAIMA:** Wannan ai shirme ne. Akwai Musulmai fa da dama masu wasannin motsa jiki a ko’ina a cikin duniya. Layla, minti nawa muka yi ne kafin mu gama zagayen?

**LAYLA:** Minti uku da sakan ashirin da ɗaya da dubu takwas.

**SAIMA:** Ba laifi! Kin ga ki gaya wa wancan ɗan’uwan naki ya kama gabansa. Wannan abin da yake yi ba daidai ba ne!

**LAYLA:** Kai, na sha fama da shi a kan haka. Kamata ya yi a ce Hassan ya fahimci cewa Musulunci bai hana wasanni ba. Ko da yake Saima, Hassan yana da ’yar gaskiyarsa fa. Akwai dokoki game da irin abin da mutum ya kamata ya sa, da kuma yadda ya kamata ya suturta jikinsa, da yadda ya kamata ya yi wanka.

**SAIMA:** Kin ga fa Layla, duk hannayenki da ƙafafunki da kanki a rufe suke ruf, kamar nawa.

**LAYLA:** E, haka ne amma kin san akwai zafi sosai. Dubi yadda muka yi sharkaf da gumi.

**SAIMA** Ya kamata mu nemi malamin da yake koya mana motsa jiki nan ya ba mu dama mu sa sababbin kayan wasan nan da aka yi saboda mata Musulmi. Ba su da nauyi, don hijabinsu iyakarsa kafaɗa, ga shi kuma an maƙale shi a wuya daga baya, kin ga

kuma sun dace da Musulunci. Game da canza kaya kuwa, kawai kya iya zuwa gidanmu ki canza a can.

**LAYLA:** Amma ai kuma hakan zai sa a yi ba ni wajen nishaɗi da maganganu da wasanni da mukan yi idan muna wanka. Haba ke kuwa! Ke ma ai Musulma ce, ke me ya sa ba kya damuwa don waɗanda ba Musulmi ba sun gan ki?

**SAIMA:** Ai mu gidanmu ba masu tsattsauran ra'ayi ba ne. Ni babata ma fa tana ganin kasancewar mutum mace, wani ƙalubale ne na yadda zai fuskanci babakeren maza da suke yi mana a wannan zamanin nan. Don muna Musulmi ba wai zai hana mu tashi mu ƙwaci 'yancinmu ba!

**LAYLA:** Ni wannan bayanin naki ba wani abu da zai hana. Yaya zan yi da Hassan da kuma irin abokan nan nasa na makarantar Islamiyya? Kai wannan makaranta tasu sun cika tsanani.

**SAIMA:** Ke ƙawata, in za ki tashi, ki tashi! Ki yi fito-na-fito da su. Ai su ba mala'iku ba ne. Wannan ƙanin naki shekararsa goma sha biyu fa kacal. Ya kamata ki gaya masa ƙasashe irin su Falasɗinu da Jodan suna da ƙungiyoyin ƙwallon ƙafa na mata. Ba sa karya wata doka ta addinin Musulunci, haka ke ma!

**LAYLA:** Sai da na nuna masa hoton matar nan na ajinmu, wato Nawal El Moutawakel wadda ita ce mace ta farko Musulma 'yar Afirka da ta ciyo zinari a gasar *Olympics* da aka yi a Los Angeles a shekarar 1984. Kin san wannan babbar nasara ce fa! Ni ma burina ke nan, wato na zama zakara a gudun tsallen baɗake na mita 400 na gasar *Olympics* mai zuwa!

**SAIMA:** Ja mu je Layla! Ke! Mu kasa tsere daga nan zuwa ɗakin sauya kaya!

**MAI BA DA LABARI:**
Shi kuwa Tafida, idonsa na kansu lokacin da suka sheƙa a guje. A halin yanzu dai ƙarshen mako ya gabato. Dauda yana shirye-shiryen zai ziyarci ƙauye wajen babansa tare da Fada Bana. Tun da shi Fada Bana da 'yan'uwansa duk za su yi murna da zuwansa, haka shi ma Dauda a matsayinsa na shugaban ɗalibai na wannan kwaleji na yanzu.

**Fitowa ta 3: A ƙauye a waje**
Maigida Ranau

**MURYAR MAZA DA MATA MANYA:**
Barka da zuwa! Sannu da zuwa Fada Bana! Sannunku da zuwa Dauda, sannunku da zuwa! Maraba! Lale!

**MAIGIDA RANAU:** Fada, Dauda, ku shigo mana! Sannunku da zuwa! Bari a kawo muku ruwa!

**Fitowa ta 4: A ƙauye a cikin ɗaki**
Maigida Ranau, Fada Bana, Dauda

**MAIGIDA RANAU:** Yauwa! Sannunku da zuwa! Ku shigo! Bari a kawo muku ruwa. Ga wuri, ku zauna, ku sha ruwa!

**FADA BANA da DAUDA:** Madalla, mun gode.

**MAIGIDA RANAU:** A to Dauda, me mutum yake yi idan ya zama shugaban ɗalibai?

**DAUDA:** Babban abin da muka sa a gaba shi ne mu kafa Kungiyar Muhawara ta ɗalibai. Ka san ina… ina wannan aikin ne tare da Layla Umar.

**MAIGIDA RANAU:** Uhmm. Ka san zuriyar Umar ɗin nan fa su ne manyan abokan gabanmu. Ka san ba ga-maciji a tsakaninmu da su.

**DAUDA:** Kai! Ban sani ba. To a kan me, Baba?

**MAIGIDA RANAU:** Fili mana. Ai rigimar a kan fili ake yinta. Kuma har yanzu a kan haka ake yi.

**FADA BANA**: Ita wannan Kungiyar Musulmin tana so ta gina sabon masallaci, mu kuma muna so mu gina sabuwar coci. Ni da wannan Isma'ila Umar ɗin mun yi aiki a kwamitin ci gaba, wanda kuma mun yi ta sa-in-sa da shi a kan ko waye yake da ikon yin abin da yake so a filin.

**DAUDA:** To, me kuma ya shafe mu ni da Layla a wannan al'amari? Mu fa ba abin da ya shafe mu. Ni shugaban ɗalibai maza ne, ita kuma shugabar ɗalibai mata, kuma an ɗora mana alhakin kafa sabuwar Kungiyar Muhawara ni da ita. Ita kuma shugabar makarantarmu tana so mu yi nasara a kan wannan aikin da ta ba mu. To yaya zan yi ne?

**MAIGIDA RANAU:** Haba Dauda, ni ba zan hana ka aiki da Layla Umar ba, amma sai dai iyakarsa makaranta kawai. To wai shin, faɗa min, ita kyakkyawa ce ne?

**DAUDA:** E, ai kyakkyawar gaske ce!

**MAIGIDA RANAU:** Af, to to to! Na gane!

**FADA BANA**: Ni fa Dauda zan fi so a ce ka fi mayar da hankali ga harkokin coci.

**DAUDA:** Haba Kawu! Ai ba maganar coci ake ba ma. Ni fa shekarata goma sha bakwai kacal. Ni ba wani abu da nake shawarar yi tukuna. Ni yanzu karatu nake, a kuma kwalejin nake da ta tara masu addinai dabam-dabam. Abin fa da kake so ke nan, Baba. Ai kai ma ba ka cusa kanka cikin harkar coci ba, tun da ga shi matanka biyu.

**MAIGIDA RANAU:** Gaskiyarka. Na yi hakan ne a matsayina na shugaba. Ka san a wurin mutanena, haka ya kamata na yi, koma na ƙara da ta uku. Haka babana da kakana suka yi. Yin hakan shi ne alamar iko da albarka.

**FADA BANA**: Ai ni tuni na haƙura wajen ƙoƙarin sa babanka ya zama mai bi. A matsayina na mai gudanar da harkokin coci, bai kamata na yi aure ba. Gara mutum ya mayar da hankalinsa a kan harkokin da suka shafi ibada. To fa Dauda, ka ga yadda 'yan'uwan juna biyu suka zama mabambantan aƙida.

**MAIGIDA RANAU:** Ka ga kuma wannan bai taɓa haɗa mu ba. Kai ma Dauda, kana da dama ka zaɓi abin da kake so a rayuwa, amma wajibi ne a kanmu mu ga cewa ba ka yi zaɓen tumun dare ba.

**FADA BANA**: Sannan kuma kada zaɓen nasa ya saɓa da ƙa'idojin zuriyarmu.

**DAUDA:** To mene ne shawararka?

**FADA BANA**: Ba kai ba ita in har an tashi daga makaranta. Kada kuma ka gaya mata kome game da harkokinmu, ko ba haka ba?

**MAIGIDA RANAU:** E to, ka san mu fa aikinmu a tsakanin al'umma shi ne mu tabbatar da zaman lafiya, ba mu kawo hargitsi ba. Ina jin ya zama wajibi a kan Dauda da Layla su nuna shugabanci na gari, kuma su nuna cewa, makarantarsu ba ta yi zaɓen tumun dare ba, a kan muƙaman da ta ba su na shugabancin ɗalibai.

**DAUDA:** To, in ko haka ne ya kamata mu nemo hanyar da za mu warware wannan rashin jituwar da ke tsakaninmu.

**MAIGIDA RANAU:** Shugabanni na ƙwarai ba abin da suke sai ƙulla zumunta. Lalatattun shugabanni kuwa ba wuya su haddasa gaba a kan ƙabilanci, ko jinsi, ko ma addini. Anya ya kamata mu bar haka tana faruwa a garin Sodangi? Mu sa ido Musulmi da Kiristoci na gaba da juna, kuma suna fakewa da addini a kan fili kawai?

**MAI GABATARWA:**

Wannan shi ne ƙarshen shirinmu na "Ji Ka Karu" a yau. Layla dai ta yanke shawarar ci gaba da guje-gujenta na motsa jiki, yayin da shi kuma Dauda yake

fuskantar wata sabuwar matsala. Sai ku biyo mu a shiri na gaba domin jin yadda za ta kaya a cikin wasan kwaikwayonmu mai taken "Haɗin kan mutanen Sodangi", inda za mu ji yadda Dauda da Layla suka sami kansu a cikin tsaka-mai-wuya a dalilin zamansu abokan juna. Idan kuma kuna son ku yi tsokaci ko kuma ku sake saurraron shirin, kuna iya tuntuɓar adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.